"Jamal! Rai a bace yake magana Jalil in dai magana ce kan yarin- yar nan karka karah yimin ita, na barka lpy.

Cikin mamaki da al'ajabi Jalil ke kallan dan uwan na shi. Anya kuwa shi ne? to mai yake damun shi?. Ko dai santa ya keyi?.

Ya rasa mai bashi wannan Amsar dan haka ya yi shiru abun shi.

KANO

Jamal ne ke ta sauri zuwa officer din Tahir.

Sallah.

Kawai ya yi.

ba tare da izinin ba ya shiga duba computer din shi. Rai a matukar bace, sbd ya rasa daga ina matsala take.

Tahir! Ne ya fito cikin daga Toilet ya xubawa ogan na shi ido.

ko bai faɗa ba yasan abun da ya ke dubawa, dan ko bai zuba shi zai je.

"Tahir! mai nake gani haka a cikin wannan Company nin wane ne ya zari wannan kuɗin haka". "Wallahi Jawad yadda ka gani nima haka na gani, kuma yan xu nima nake shirun zuwa na sanar ma", amma wani hanzari ba gudu ba kasan wane ya ciri wannan kuɗin? Papy ne ya cire su ta wani sabon account da ya buɗe yan zun nan na gano haka.

Amma bari na nuna maka, take ya nuna mashi rai shi ya kuma bacci ya kasa furta ko uffan kai wai ya fuce.

Kai tsaye officer din papa ya wuce rai bace.

Sallah ya yi ya bashi damar shigowa, gaida shi ya yi.

Ya amsa. Tare da tambayar sa ko lafiya ya ganshi haka. "papa kayi hakuri da abinda zan faɗa maka, "bakomi ina jinka"

Papa mai yasa papy  baya sanka? Mai yasa kullum muradin shi ya dinga tuzar ta ka? Mai yasa baya san ganin ci-gabanka? Mai yasa kullum muradin shi ya tarwa tsaka?

Kafin ya kuma wata maganar tuni papa ya da ka mashi wata gigitacciyar tsawa. Ya ishe ka haka Jawad ka she baka da mutum ci? Ni xaka kallah ka dinga zagin dan uwa na a gaba na.

Na san abun da kake san sanar dani Jawad ka kiya ye dan zan iyya komi sbd dan uwa na, kuma ko Company nan zai tarwatse babu ruwan ka da shi kayi aikin ka, ko kuma  ka koma wani Company nin.

Jawad ya shiga bawa mahaifin na shi hakuri tare da fice wa ya barshi.

Yau da wuri suka shirya dan fita kai Jamal makaran. A bakin comput din gidan suka tadda ta da alama su take jiran, tayi shigar ta kamar yadda ta  saba.

Mota suka dauka suka fito da ita.

Dai dai lokacin kuma dad ɗin ta ya fito ya ce  dan Allah Jalil ka kai Jamal makaranta Jalil xamu fita tare zai kai ne airport kuma ina sauri ne kaga sai ya dawo da mutar.

" Tom shikenn  ba damuwa dad tare da gaida shi".

Motar ya shiga. Ita ma tabude gaban motar ta shiga da mamaki ya ke kallan ta amma bai yi magana ba.

Suka dauki hanya "dago wa tayi ta kalle shi a nutse sannan ta ce yaya Jamal ina kwana. " kallan ta yayi kafin ya ce kin tashi lpy,  lpy kalau Alhmdllh yaya Jamal.

Daga wannan babu wanda ya kuma ce wa kowa komi har suka kusa kara so wa makarantar. Wata iska ce ta taso da guguwa wadda gaba daya gari yayi duk abun ka da lokacin damuna. Jamla cikin tsoro da gigita ta fada jikin Jamal ta saka kanta a kirjin shi jikin ta na mugun rawa, to ni likaf din dake fuskantar ta ya fice ya kama gaban shi. Shi ma tsaida muta ya yi sakamakon baya ganin hanya.

Cikin ikon Allah iskar ta Farah lafawa. Alhmdllh gari ya farah haske. Jamal ya dago idon shi ya sauke su kan jamla data rungume shi ta kuma saka fuskantar ta a kirjin shi.  Kasa mata magana ya yi ko ya ce ta dago har gari ya yi haske kowa ya farah cigaba da tafiya.

Cike da sanyi murya ya farah magana, kina so ki makarah ne. Kawai abinda ya ce mata kenan.

Cike da jin kunyarsa ta dago kanta daga kirjin shi, cikin rudewa ya ke kallan ta amma ya kasa furta ko uffan,  innalillahi,wainna illaihiraju ya kafar maimai tawa cikin zuciyar shi. Ya zuba mata

ido sai kallan ta yake yi, tuni ida nun shi sun canza da bari zuwa jah, ya kuma kasa furta ko da alifun.

Cikin nutsuwa ta dai-dai ta zamanta sannan ta kalli hanya.

"Yaya Jamal! ta kirah sunan shi dan Allah kayi hakuri kaji.

Bai iyya furta mata ko uffan ba ya yi karfi halin cigaba da tafiya a bakin school din su ya ajeta.

Jiki ba nauyi ta fita sbd ta tsorata da yanayin nashi a tuna nin ta sbd ta rungume shi ne.

Har ta shiga makarantar ida nun shi kanta, tabbas wannan ba jawahir d'un su bace sbd fatan ta ma ba iri ɗaya ba ce amma tabbas suna matukar kama, tabbas akwai wani boyayyen Al,amari a tsakanin su.

Tom ko dai ya tabbata jawahir wannan yar uwar tace, to kuma akai mama ina? .

Shi kaɗai yake kiɗan shi yake rawar shi.

Tun da ya koma parking motar kawai yayi ya kama gaban shi, zuwa gida sbd kan shi da ke mai wani dan karan ciwo wanda da'yar yake bude idon shi.

Ya na shiga gidan kwanciya ya yi wani zazzafan zazzaɓi ya rufe shi wanda jikin shi har rawa yake yi.

Dad ya sauka garin Kano lpy ya dauki hanyar Company su. Ba jimawa suka gama cike-cike da komi sannan aka tura su kan fanin papy dan tabbatar da Agreement din. Shi da Alhaji Ahmed.

" A mota ne Alhaji Ahmed yake sanar da shi kallan karamcin ( J. U.J) company har yake ba shi labarin papa da papy ranar da suka bashi tsoro bai san 'yan biyu ba ne, dad yana ta dariya.

Cikin ikon Allah sun samu tarba ta musamman inda su ka gama tattaunawa akan komi kafin daga bisani papa ya kira Jawad dan shaida masu yadda komi ya kasan ce idan ya amince da hakan. Saka makon yau Bebyn papa bata zo ba.

Ba kuwa wani jimawa ko bata lokaci, ya shigo d'akin bakin shi dauke da Sallah ma.

Dad ne ya dago da sauri dan ganin mai sallah mar idan ba kun nan shi gizo ya masa ba yake jin kamar Muryar Jalil.

Cikin firgice da tsanani mamaki yake kallan Jawad, tabbas wannan Jamal ne babu wani banbanci ko tan ta ma.

Ya mike tsaye jikin na rawa yake kiran sunan shi Jamal, mai ya kawo ka nan kuma

Typing 📲

GAYYA CE!

*Free page*

*Written by*

*Fatima alaramma lafazi*

*(Falaramma)*

*Sadaukar kar wane ga Sadiq Abubakar CEO din lafazi Allah ya Kara masa lpy, da nisan kwana mai albarka, godiya ta musamman*

💖✨✨✨💞💋💋

Wanan sabon littafi ne, dana farashi kwanan, ina rokon Ubangiji ya bani ikon gamawa lpy, ina rukun Ubangiji ya bani da mar rubuta abun da mutane zasu amfana dashi wannan kenan.

✨✨✨

Wannan labarin na musamman ne ba gama garin labari bane, GAYYA CE! kuna ji kun San abun sai Wanda ya karan ta, labarin ban dariya da kuma soyayya, tsan tsar cin amana da kuma Butulci, San zuciya da kuma hassada, duk acikin book din GAYYA CE! kunaji kun San ba karya littafin, ina alfahari da ku sister's nagode.

Pg 11-12

...............Kallan shi Jawad ya ke cikin nutsuwa ba tare da ya ce mai ko kalah ba. Cikin sanyin Murya ya farah mashi magana, Alhaji ka zauna muyi magana cikin nutsuwa da fahimtar juna.

Haka Dad ya zauna jiki ba kwari sai dai abun har yanzu yana cikin ran shi dan ya kasa saita kan shi. Ya kuma zubawa Jawad ido yana ta mashi Kallan k'urillah  dan so yake ya gane wannan ba jamal da gaske bane.

Cikin nutsuwa suka Farah magana inada Dad ke sanar dashi labarin su Jamal, da kuma yadda suke kama.

Bayan sun gama  magana ne papa ya ce ba komi ai kowa ne bawa ance kalar shi 7 ce dan haka babu, mamaki.

Shi kuma dad yayi alƙawarin kawo musu su Jamal dan su tabbatar da abin da yake faɗa, dan yaga basu ɗauki zancen da mahimmanci ba. Haka dai suka gama kowa ya kama gaban shi.

Shi kuwa  bangaren papy duk jikin shi yayi sanyi da jin wannan mummunan labarin, yana ta addu'a Allah ya sa ba,abinda yake tuna ni bane. Gashi yau tsawon shekaru goma kenan raban shi da doctor Aminu.

............ Jalil ne ya shigo d'akin bakin shi dauke da Sallahma  bai karah furta ko uffan ba sbd hango ɗan uwan shi da ya yi cikin wani mawuyacin hali. Da gudu ya karah sa gaban shi yake tan

bayar shi mai ke damun sa amma ya kasa magana, fita ya yi ya samu Napep aka dauke shi zuwa wani privet hospital, ba kuwa b'ata lokacin aka shiga dashi.

Kusan 10 minit ba wani labarin.

Ya kai wajen 30minit wani doctor ya fita ya ce ya biyo shi office.

Suka zauna kusan a tare, doctor ya zubawa jalil ido yana kallan shi yana sakar mai murmushi kafin ya farah magana. Jikin na shi da sauki sosai munyi masa injection kuma in sha Allah zai farka nan ba da jumawa ba. Ya kare maganar fuska dauke da murmushi.

Nagode sosai doctor, Amma ina katin magungunan yake, doctor ya nuna mashi takardar gaban shi da hannu, sannan ya ce karka damuna biya komi. Jalil ya kalleshi da mamaki amma kafin ya yi magana ya ce na kasan ce ina matukar san 'yan biyu a rayuwa ta sbd nidin ma 'yan biyu ne lokacin da muka girma d'an uwa ne ya rasu, wannan aikin da nake ma nashi ne nake mashi sbd ina matukar girmama ra,ayin shi idan babu damuwa ina san muzama Abokai ko in ce Aminai, ya kare maganar murya a kausashe.

Tom shikenn babu damuwa Ubangiji ya sa muzama Alkairi ga junan mu na gode sosai fa, ya mike dan fice wa dan hankalin shi na kan ɗan uwan shi.

Doctor faruk ne ya rako shi har d'akin in da sukayi sa,a kuwa ya farka, tare suka Farah jerah masa sannu inda ya dago fuska dauke da murmushi yace ai Alhmdllh naji sauki ma ina ga zamu iyya tafiya dan yasan bawani kuɗi ne a hanun Jalil ba. Doctor ya karah matsowa kusa da shi yace yanzu mai kake ji, ya ce ba komi Alhmdllh, "ma sha  Allah Ubangijin ya baka lpy my bro, batun sallah ma kuma ka ajeta dan bazan sallameka yan zu ba sai na tabbatar da samun lafiyar ka.

"Jamal doctor sam bana san zanman hospital din ne fa, doctor ya dafa shi tare da rike hannun shi, dan Allah ka kwantar da hankali ka, Ni she is my brother zan kulah da kai kuma ina san lafiyarka.  Haka dai suka cigaba da tattaunawa har Jamal ya yadda da maganar Farouk da kuma abotar su dan ya fahim mutum ne na mutumci kuma ya fahimci d'acin da yake ji na rashin dan uwan na shi.

Jalil ne ya koma gida dan sanar da su inna hankali su yayi matukar tashi inda Jalil ya kwantar masu da hankali sannan suka tahu Hospital din.

Jikin nashi da sauki Alhmdllh suna ta hirah da shi inda minti 15 biyar duk ya na shigowa yaga jikin Jamal ɗin da, ga kuma tsantsar nuna soyayya ga Alhalin nashi.

............. Alhmdllh an faka kasuwanci mai kyau tsakanin ( J U J ) company, da  (M K J) company inda su Dad zasu dawo gida Kaduna.

Inda shi kuma dad ya dawo da kudirin kawo su Jamal dan ganawa.

Da misalin ƙarfe 11:30am.

Dad ya sauka garin Kaduna zuciya cike da faraciki ya dawo gida Kaduna, a airport ya kirah Jalil dan yazo ya dauke shi, yace gashi nan zuwa.

Ba kuwa b'ata lokacin yazo ya dauke shi inda yake faɗa mashi ai Jamal ne bashi da lafiya yau kwana 2 yana kwance a hospital, sosai Dad yaji rashin jin dadin hakan inda ya ce da yamma idan ya huta zai zo duba shi, dai dai nan kuma parking a comput d'in gidan, inda ya raka shi har babban falon gidan sannan ya yi masa sallahma.

B'an garen Jamal kuma sosai yake samun kulawa baga 'yan uwan sa ba baga doctor faruk ba wanda har mom din shi da kanwar su sunzu duba shi, ya kuwa ji daɗin hakan sosai dan kuwa yadda Alkairan su suka zo, inda Fatima kanwar shi take yaba kyauwun shi da kirkisa yaya Farouk yake tsokar bar shi kaga ka bro Jamal Fatima ta faɗa.

Dad be samu damar shigowa wa hospital ba sai washe gari da safe. Yazo yaga jikin na shi da sauki Alhmdllh inda yace zai dawo da yamma in sha Allah shida su jamlah su duba shi. Amma

abin da ya bawa Jamal mamaki shi ne yanda dad keta ƙalilan shi ' shi da Jalil kamar yau ya farah ganin su.

Hakan ce kuwa ta kasan ce dan daddare dad ya kawo su suka duba shi sosai mom ke jerah mai sannu sbd ita masifar kaunar su Jawad,  yau ma harda abincin ta inda tace kullum za,adinga kawo musu. Sai dai shi Jamal gaba daya hankali shi nakan ya tambaye su jamlah amma ina kunyar dad yake ji. Kamar kuwa Jalil yasan mai yake sakawa axuciyar shi, sai kawai yajiyo Muryar Jalil yana tanbayar ina aka bar jamlah, dad ya yi murmushi yace sorry Jamal tana maka sannu gobe da safe zata zo, Ni zan kai mom Asibiti ne sbd ita ba bata jin daɗi, " kallan ta sukayi cike da tausaya wa suna jirah mata ya jikin.

Sun jima suna hira daga baya sukayi sallah ma. Sakamakon ko inna basu haɗu da ita ba sbd ita da jawahir da yamma suke tafiya.

Mom  jamal ce ke gaban doctor inda take mata bayanin abinda yake damun ta sosai doctor Amini ke kallon mom fuskarta dauke da murmushi, " inda ta ce wa mom bazan ce maki komi ba Hajiya Maryam amma bari nasa ayi miki text dan tabbatar da zargina".  Haka kuwa akayi mata text inda ganta keta faduwa dad yana ta kwantar da hankali ta in sha Allah ba wata matsala ba ce.

ku san mitina 30 suka dauka sannan aka dawowa da doctor Amina result din ta kallah " ta ce zargina ya tabbata. Dad ta kallah tace Alhaji ina tayaka murna dan Hajiya na dauke da ciki wata biyar ajikin ta, mom kuwa cikin damuwa da fargaba take kallan doctor "tace cikin kuma doctor da girma na haka kin san rabona da haihuwa kusan 20 years kenan, bata kai ga wata maganar ba

dad ya rufe mata baki rai a bace ya ce haba Hajiya Amina Maine haka. Ni ina matukar farincikin da wannan cikin a gaban ta yayi wa Ubangiji sujjada, ta farincikin tare da bawa doctor kyau ta sannan ya jata suka tafi.

Ni kuwa nace Ubangijin ya azurta ku da naku mom.

Tun a mota dad kewa mom nasiha sbd gaskiya bata wani ji dad'i wanna cikin ba dan ta gama haihuwa.  Amma a nasihar da dad ya mata sai ta gamsu kuma ta godewa Allah.

Fatima ce yau ta Farah zuwa hospital da kayan breakfast  din su, dakin ta shigo dan kuwa lokacin yayi wanka ya shirya shaf ga wani farih da ya karah da kibah sbd yana matukar samun kullah wa ta ko,ina. Yana san a sallah me shi amma fafur doctor yake dan kullum tare suke kwana da shi da Jalil a gurin sa.

Bakin ta ɗauke da Sallah ma ta shiga ya amsa mata fuska a sake sbd yarinyar tana matukar burgeshi sbd nutsuwa ta. "Yaya Jamal ya jikin naka", ina fatan  da sauki dan mom ma tana gaida ka". Da sauki Alhmdllh Fatima ya mom na fatan tana lpy?"  Lpy lau take yaya Jamal.

Haka dai suka dinga hira sama sama, inda tayi saving na shi ta mika mashi, " ya barb'a tare da mata godiya.

Yaya Jamal ina yaya Jalil yake naga ban gane shi ba?,

Yaje kai jamla makaran ta ne.

Amma nasan anjima zai dawo bazai dade ba in sha Allah.

Shiru ce ta biyu baya.  Kusan 10 minit.

Sallah mar yaya Farouk ce ta saka su amsawa, fuska ɗauke da murmushi duk kan nin su.

Doctor Farouk ya zauna gefen Jamal sannan ya farah jirah masa tambayoyi yi kamar yadda ya saba,  yana bashi amsa.

Bro Farouk dan Allah ka sallameni  ko badan niba ka duba kaga yadda Jalil yake ta wahala shi kaɗai duk ya yi baki ya rame.

Pulet din hanun Fatima ya karba da cup sannan ya farah kaiwa bakin shi yana murmushi, Bro jiyafa ina kallan ka yadda ka kurah wa Jalil ido kana kallon shi, karka damu har yanzu babu wani banbanci a tsakanin ku, amma nayi maka alkawarin zan sallame ka nan da kwana biyu.

Suna kai wa nan Jalil yayi Sallah ma shida Jamla.

Guri ta nema ta zauna sannan ta gaida su ɗaya bayan ɗaya ta kuma yiwa Jamal sannu da jiki, daga haka bata kara cewa komi ba amma abu d'aya ne ya bata haushi yadda Fatima ta dare suna ta kwasar hira ita da Jamal, dan har zuciyatar ta zafi take mata tayi matukar kewar Jamal ɗin.

Fatima da doctor Jalil ne suka fita zuwa office din doctor.

Yana fita jamla ta sauke wata ajiyar zuciya mai karfi. Tare da dage rikaf ɗin dake fuskarta.

Tashi tayi ta jawo pulet ta hau zuba mashi sakwarah da miyar Agushi wadda taji na ma kawai kan shi take yi. Ta miƙa mashi batare da tace nashi kallah ba.

Kallan ta yake cike da mamaki ya rasa mai yasa yake jin mutuwar jikin indai yana tare da ita. "Yaya Jamal gaskiya ka ce sbd yau ton  asubah na tashi nake haɗa maka naso dashi zaka karya amma babu yadda na,iya.

Tana maganar ne ranta a matukar bacce, dan ya tabbatar da abinda yake gani a idonta ne yasa ya ce,"to ai hanuna ne yake mun  ciwo bazan iyya ci da kai na ba ya kare zan cen yana wani kyakkyawan murmushi.

Matsawa tayi gaf da shi ta ce maza bude bakin na baka, "cikin  tsoka na yace babba dani zaki bani abincin a baki," hade rai tayi ka bude ina jiran ka. Haka ta dinga bashi yana ci yana kallan fuskarta ciki da santa da kaunar ta.

Yaci abincin sosai sannan ya ce mata ya koshi, yana ta yaba daɗi abincin, sai daɗi ta keji,

Tsokanar  ta yake wai dama haka kika iyya badah abinci a baki ban sani ba?.

Tana jin shi ta mai banza dan ta fahimci tsokanar ta yake yi.

"Zo kiji" taji Muryar shi daga sama.

"Wai  ni yaya Jamal baka san sunana bane?.

Ohhhhh sorry Noor, ta k'ara so  inda yake, mai yasa yau bakiji makaranta ba?.

Kasa tayi da kanta sannan ta ce nace yau zan zo na duba ka ne, shiyasah ban je ba,

"Tom bakuda lecture ne?

"Eh babu, duk wanda muke dashi ready na iyya"

Hira su keyi cikin nutsuwa inda yake addu,ar kar Allah ya kawo wani yaga jamlah dan bai shirya wa tashin hankali yanzu ba. Ya jiyo Muryar inna tana ce wa yanzu na zo Farouk.

Ta d'urah hanunta kan Handel din k'ofar, nan ma hankali  shi ya karah tashi dan bai san yadda zai yiwa Jamal maganar ta maida likaf dinta ba.

Typing 📲

GAYYA CE!

*Free page*

*Written by*

*Fatima alaramma lafazi*

*(Falaramma)*

https://youtube.com/@fatimaalaramma?si=v_EK6JyH_nkqroPZ

*Sadaukar kar wane ga Sadiq Abubakar CEO din lafazi Allah ya Kara masa lpy, da nisan kwana mai albarka, godiya ta musamman*

💖✨✨✨💞💋💋

Wanan sabon littafi ne, dana farashi kwanan, ina rokon Ubangiji ya bani ikon gamawa lpy, ina rukun Ubangiji ya bani da mar rubuta abun da mutane zasu amfana dashi wannan kenan.

✨✨✨

Wannan labarin na musamman ne ba gama garin labari bane, GAYYA CE! kuna ji kun San abun sai Wanda ya karan ta, labarin ban dariya da kuma soyayya, tsan tsar cin amana da kuma Butulci, San zuciya da kuma hassada, duk acikin book din GAYYA CE! kunaji kun San ba karya littafin, ina alfahari da ku ges nagode.

Pg 13-14

........Cikin hanzari ya ce ashhhhhh  tare da haɗa fuska kamar wanda wani ciwo ya taso ma shi.

Cikin sauri ta karah so inda yake tana tanbayar shi ko lafiya, da sauri ya riko ta ya sauke likaf din cikin dabarah batare da ta fahimci hakan ba.

Sannu yaya ko na kirah ma doctor ne, ya d'aga mata ido alamar eh, har zata fita yace amma dan Allah karki karah daga likaf din nan.

Abakin kofar su kayi karo da inna inda har kasa ta tsuguna ta gaida ta, cikin girmama wa, sannan tayi gaba abin ta, inna cikin mamaki da kad'uwa ta ke kallan ta sbd jin Muryar ta tamkar jawahir din ta data baro a gida. Jiki ba nauyi ta shiga d'akin  baki dauke da Sallah ma, ya amsa cikin sakin

fuska tare da nuna mata guri ta zauna, ya gaida ta ta amsa tare da tambayar jin nashi, "yace Alhmdllh".

" Nace jamalu wannan yarin yar da ta fita Ni kam wacce ce ita?, jiyayi gaba shi ya faɗi dan jin kalmar ta amma ya ɗan dake yace inna Jamal ce fa yar gidan Alhaji. "Ohhhhh Ni dai yarin yar tamun yanayin murya da jawahir wllh", ta kare maganar cikin jimami.

" Kai inna abu ne naku na tsufa amma yan she zaki haɗa ta da yarki. Ya faɗa cikin salon tsokana.

"Inna to yar yawa bata fita komi ba jamalu, na tabbata da ace jawahir ke samun kulawar yarin yar nan da tuni tafi haka kuma sai an kalleh ta an kuma kallan ta. Dariyar Jamal ya yi sbd yasan dama za,ayi haka, yace kai inna banda sanka fa. Nan dai suka dinga yi.

Fatima ce zai ne gaban Jalil wai nace yaya Farouk taya kake banbance yaya Jamal da yaya Jalil, Ni dai gani nake kamar bazan iyya gane suba. Dariya ya yi mata Sannan yace nima fa ba sosai ba nake gane su Fatima, Jalil ne ya juyo yace kina so kidinga kage mu, tom kawai ki zauna ki fahimce mu sosai zaki gane mu, sai kuma kaf d'in su kasa dariya.

Akwan a tashi ba wuya a wajen Allah gashi yau watan Jamal biyu da Sallah mushi a hospital. Sosai yan zu Farouk ya zama abokin su Jamal dan har zuwa gidan su Farouk suke su sha Shira da mom musamman Jalil, wanda a wannan lokaci sukayi wata muguwar shakuwa da Fatima. Inda ita kuma bikin ta kullum yake karah matsowa inda yan zu saurah sati Daya.

Sukuwa su Jamal tuni chanji rayuwa ta same su dan yanzu Allah har gida faruk ya bawa su Jamal kyau ta, suke zaune.

A yanzu idan kikaga Jalil da Jamal zaki dauka wasu masu faɗa ajine ne dan ko suturar da suke sawa ta chanza. Sosai suke kama kuɗi sbd Jalil ma ya koma kasuwa mom Farouk ta d'urah shi kan duniyar ta sbd ta yadda da amanarsa inda shi kuma Jamal ya koma kan sana,arshi ta funichace dan sosai yake samun kasuwa dan bai yarda ya zauna kasan wani ba.

Inda Jamal yakoyawa jamla mota sosai ta iyya dan yanzu da kanta take zuwa makaranta ga kuma wata matsananci yar soyayya data kullu tsakanin su, sai dai babban tashin hankali Jamal shine kada dad ɗin jamlah ya hana shi ita. Amma a zahirin gaskiya yana matuƙar kaunar ta. Koda yaushe yana san ya sanar da ita halin da ake ciki na kamar su da jawahir kan war shi amma ya kasa, sbd gudun abinda zai faru.

Jamal ce ke shirya wa cikin wata shaddar Farah wadda Jalil ita ce yasa da safe kafin ya fita ya saka, tayi masa matukar kyau, sannan ya fito zuwa falo inda ya tadda su Farouk da Jalil yasan fa yanzu zasu ce zasu bishi dan haka ya haɗe rai yace. Jalil ya bashi mukulin Babur zai fita, wani kallo Jalil ya watsa mashi sannan ya ce wllh yau duk inda zaka kafarka kafarmu sai muje Farouk ya ce bako shakka duk da nasan ba bazai wuce wajen jamla ba, wadda yake ta raina mana hankali wai basan yake ba, wanda nid'in na dade da sanin hakan.

Banza ya musu ya fice suka bishi inna da ta shigo falon yanzu ta bisu da Allah ya tsare.

Shi kuwa da'yar ya yarda suka tafi tare musu iyyakar inda zasu tsaya. Suka ce sunji ba komi zasu tsaya a inda ya ce, amma a zuciyatar su basu Amince da hakan ba.

Bakin k'ofar gidan su jamla sukayi parking sannan suka shiga, tafiya sukayi kaɗan ya ce ku tsaya anan, na shiga na fito. Bai k'arah sa maganar ba ya hango ta tana doso su, inda shi kuma Jalil ya tsirah mata ido shida Farouk suna kallan ta.

Tabbas ita ce wannan jawahir ce, sautin Muryar ta ce ta dawo da su cikin hayyaci su, baki na rawa yace jawahir mai ya kawo ki nan kuma.

Fuskar ta ɗauke da murmushi tace yaya Jaml dai. Dan shi bai ma kawo wata jamlah ba ce.

Jamal ne ya jawo su yace ku dalla can wannan ce fa jamla, kawai suna kama ne, dan Allah malam ka kama kanka ya ce wa Jalil.

Ko kallah shi Jalil bai ba yaje gaban ta ya tsaya ya ce. Ki faɗa tsakani da Allah ke ba jawahir ba ce. "Baki da mamaki ta ce Allah yaya Jalil jamlah ce ni. Cikin sanyin jiki ya farah mata baya ni inda ta gamsu da maganar sa, ta kuma yi masa alkawarin zata zo gida taga jawahir da wannan sukayi sallah ma dan kan shi ya farah masa ciwo.

Kai tsaye gida suka koma inda kawai kwanciya ya yi sannan sukayi sallah ma da Farouk dan shima jikin shi ya yi sanyi.

*KANO*

A yanxu wani takun sak'a ne ya shiga tsakanin papy da Jawad dan sosai ya gane halin shi da kuma san, cutar da shi da yake ƙoƙarinyi, cikin wannan week din ne ma yasa aka tsinka mashi

birkin mutar shi da'yar Allah ya taimake shi ya fita lpy daga mutar, kuma yasan wanann Baya rasa nasaba da papyn dan yanzu baki d'aya ya tsane shi.

Ita kuwa Bebyn papa bata san duk abinda yake faruwa ba kuma Jawad bai canza mata ba sbd ya fahimci tana san cigaban sa dana mahaifinsa dan haka shima ya bata girbi na daban a zuciyar sa.

Shi kan shi papa ya rasa mai ke damun d'an uwa nashi, gaba ɗaya.

Nasara kam sosai ake samun ta, inda papa yake gina wani k'atan family Hausa wanda yake ta cinye mashi kud'i, kuma a yan zu ya na gaf da kammala shi.

Ina da sukuwa su Ammy rayuwa suke ta farincikin da jin dadi sbd ɗan ta ya samu farincikin duk da har yanzu bai wani fiye magana sosai ba amma haka ma ta godewa Allah.

*Kaduna*

Yau kwana biyu da zuwa gidan su jamla inda tun daga wannan rana Jalil ya fita daga lamarin Jamal.

Shi a tunaninshi babu wani abu da ɗan uwan na shi zai boye mashi amma sai yaga sabanin hakan. Dan haka ya kama kan shi.

Shi kuwa jikin shi duk ya yi sanyi, shi kan shi yasan bai kyautawa ɗan uwan na shi ba, amma ya yi hakan ne dan gudun abinda zai je ya dawo.

Yau ma yana shigowa d'akin ya tashi zai fita ya rike mai hannu, Jalil dan Allah ka saurareni, dan Allah kayi hakuri nasan ban kyauta maka ba amma kayi hakuri kaji.

"Ummm idan ka gama ka sake ni zan tafi malam.

Haka dai ya yi ta bashi hakuri Sannan ya ce bakomi Allah ya sa haka ne yafi Alkairi, tare da fice wa ya barma shi dakin.

Gobe ne ya kasan ce dauren auren Fatima.

Da Jalil da Jamal ake yin komi, sai dai a daren ne Fatima ta kira Jalil tana kuka tana faɗa mashi ita ta fasa auran shi, sakamakon wani video da aka turu mata nasa. Shima kuma da yaga ni yace karta damu zaizo gidan yanzu in sha Allah.

Sanar da Jamal ya yi halin da ake ciki sannan suka fice zuwa gidan su Farouk din dan samun abokin na su da maganar.

Cikin sa,a suka same shi inda sufa Farah tattaunawa kan matsalah. Abun ba karamin batawa Farouk rai ya yi ba dan sunyi binciken halin shi amma basu gane komi ba.

Tuni mom ta san da batun dan haka a falo suka same ta ta zagba tagumi. Gaida ta sukayi kamar yadda suka sabba, sannan suka shiga jajanta lamarin inda mom kallo ɗaya zakayi mata ka fahimci ta shin hankali dake tattare da fuskrta.

Take ta kira kanin mahaifinsu suka sanar da shi bai jima ba yazo da yake ba su da nisa, haka dai sukayi ta tattaunawa, da jimanta lamarin wannan shine karo na biyu da aka fasa auran Fatima, sunata tattaunawa daga baya kanin mahaifin na su ya tafi shi kan shi ya rasa maka ma.

Wani sabon hawaye ne suke zuwa kan kuncin mom nan da nan hankalin su ya k'arah tashi, Jamal ne yace mom dan Allah ki dena wannan kukan komi zai daidai ta da izinin Allah.

Fatima ce ta she go falon idon ta ya yi jajur  duk ya kunburah, gaba ɗaya ta  basu tausayi.

Gaban Jalil ta tsaya cikin kuka ta ce yaya Jalil kaga abun da kebi ya yi mun ko, ta kuma fashe wa da sabon kuka.

Komawa tayi ta rungume mom suka fashe da sabon kuka kowa ya kasa furta komi acikin su.

Mom ce ta dago murya na rawa tace Jalil, "na,am. Mom sai kuma tayi shiru, tashi yayi ya koma inda take yace ina jinki mom.

"Dan Allah  jalil kayimin wata alfarma mana, dagowa ya yi jikin na rawa yace. Ina jinki mom.

Dan Allah ka auri Fatimah!!!

ka tausaya min nida 'yata kaji tausayi na. Tana kaiwa nan ta kuma fashewa da kukan.

Gaba daya jin shi da ganin sa sun ɗauke shida Jamal, hatta Farouk abu ya bashi mamaki dan bai taba zatan haka daga gare ta ba.

Innalillahi wainnailaihiraju,un!!! Abun da suke furtawa shida Jamal kenan.

Kuna ganin zai amince da wannan auren.

Typing 📲

GAYYA CE!

*Free page*

*Written by*

*Fatima alaramma lafazi*

*(Falaramma)*

https://youtube.com/@fatimaalaramma?si=v_EK6JyH_nkqroPZ

*Sadaukar kar wane ga Sadiq Abubakar CEO din lafazi Allah ya Kara masa lpy, da nisan kwana mai albarka, godiya ta musamman*

💖✨✨✨💞💋💋

Wanan sabon littafi ne, dana farashi kwanan, ina rokon Ubangiji ya bani ikon gamawa lpy, ina rukun Ubangiji ya bani da mar rubuta abun da mutane zasu amfana dashi wannan kenan.

✨✨✨

Wannan labarin na musamman ne ba gama garin labari bane, GAYYA CE! kuna ji kun San abun sai Wanda ya karan ta, labarin ban dariya da kuma soyayya, tsan tsar cin amana da kuma Butulci, San zuciya da kuma hassada, duk acikin book din GAYYA CE! kunaji kun San ba karya littafin, ina alfahari da ku ges nagode.

Pg 15& 16

..................................Jamal ne ya yi karfin halin dagowa yace mom dan Allah ki dena wannan kukan babu matsah ya Amince da auren fatima ita ma ai k'anwarmu ce bata da wani bambanci tsakanin ta da jawahir a wajen mu.

Shi kuwa jikin jalil har wani tsima yake yana kallan ɗan uwan na shi ido cikin ido amma ya hana shi Magana.

Mom ta Farah ma sa gdy da saka albarka.

Jamal ya ce bakomi mom ai duk ɗaya ne. Shi kam Farouk ma ya kasa magana sbd gaskiya bai so hakan daga mahaifiyar tasa ba.

Bayan mitina 10 kowa ya yi shiru a d'akin ba wanda ya ke cewa kowa komi, kowa da abin da yake zargawa cikin zuciyar shi.

Jamal ne ya yi karfin halin magana yace mom sai zuwa safe idan Allah ya kai mu, zamu tafi gida, zamu shigo da wuri dan tattauna wa.

"Tom shikenn Ubangijin ya kai mu goben rai da lpy Mom ta faɗa.

Farouk hannu kawai ya miƙa masubata re da yace komi ba, sukayi musabbaha sannan suka fita.

Koda suka koma gida basu wani b'ata lokacin ba suka sanar da inna da Babba ya ji dadin yadda Jamal ya karbe lamarin inada shi jalil ya kasa furta komi. Kuma Ababba ya ce Allah ya sanya alkairi da albarka. Suka kiran mom aka k'arah tattaunawa, inda ta musu godiya ba iyyaka.

shi kam ranar jalil da Jamal, basu rontsa ba.

Ban garen Fatima ma basu rontsa ba dan kwana tayi tana kuka. Yarin ya mai ilimin ta, da ajin ta, da kyauta. Amma yau ita akeyiwa wani tayin auren ta har ana haɗa shi da Allah , amma ya zatayi kowa da kaddarar shi. Ubangijin ya sa hakan ne yafi mata alkairi.

Washe gari  da sassafe su Abba da wan baban su jalil suka je gidan, suka tattauna na. Ina aka tsaida daurin aure kamar yadda aka saka karfe 10:00  na safe. Alhmdllh sunyi farincikin da wannan auren sbd dangin su Fatima muta nan kirki ne.

Asalin su Fulani Rano  ne mahaifin finsu da mahaifiyar su, kuma duk kan nin su y'an uwan juna ne, Baban su Farouk Alhaji Abubakar shine aiki ya kawo shi garin Kaduna daga nan ya zauna a garin shida matar sa mom Hauwa  sun haifi yarah y'an biyu maxa sune Farouk da Abubakar sai Fatima. Sun girma inda suke Farah karatun su Abubakar yana ɓangaren doctor inda Farouk yake business. Shekarun su Ashirin a duniya mahaifinsu Alhaji Abubakar ya rasu, inada ita kuma Fatima tana da shekara bakwai a duniya.

Bayan rasuwar mahaifinsu da shekaru biya shima Abubakar ya fara ciwon wata shida ya yi sannan ya rasu wata ranar juma'a . Inda ranar ta zama ranar baƙin ciki, Farouk kuwa sai kulleshi akayi a d'aki har ciwo ya yi sannan daga baya ya samu sauki.

Daga nan ya hakura da duk wani aikin shi ya koma na Abubakar. Wannan shi ne kaɗan daga cikin tahirin su Farouk.

*Asalin labarin*

Washe gari karfe 9: 00 tayi dai dai amma angu yana kwan ce da'yar yake juya jikin shi.

Inna da Jamal ne suka shigo  d'akin. Kwance yake ya kalli samma idon shi a rufe amma da alama ba barci yake yiba.

Gyefen shi suka zauna, A hankali inna ta riko hannun shi ta kirah sunan shi a nutse ya bude idon shi badan ya ce komi ba. Ta fara magana jalilu ina san kasan wani abu shi bawa da kake gani kowa da kallah jarrabawar shi.  Yarin yar nan mutuniyar kirkice haka zalika iyayen ta dan Allah kada ka basu kunya a matsayin ka na wanda suka Amince maka har suka baka yar su badan duba matsayinka ba , nasiha kalah kalah take yi masa a haka har ya gamsu ya kuma karbe kaddara.

"Inna tom  yan zu tashi kaje kayi wanka ka shirya, nagd wa Allah da ya nunan wannan rana zanyi surukai, suka saka dariya gaba ɗaya.

Karfe 10:00  Aka shaida daurin Auren Fatima Abubakar da jalil Ahmad  kowa idan ka kalleshi zaka hango farincikin a tattare da shi musamman Farouk da mom, shekam ango ba,a gane shi shida Jamal dan ko wanne amsa wa kawai yake yi, inda da aka samu sauki aka shiga gidan dan gaisawa da iyaye da Amarya.

Sun gaida mom da mutanen biki.

Sannan suka yi sama babban falo dan ganawa da Amarya da k'awayen ta tom da Farouk ya faɗa mata ga sunan gaban ta ke bugawa dan batasan da wane ido zata kalli yaya Jalil din ba.

Inda su kuma kawa yenta suka ishe ta da zasu ga angon da ake boye musu kawai sai tayi murmushi.

Suna zaune anata tsokanar shi yana dariya, dan tuni ya saki jiki ba yasan ya nuna mata komi ko mita ne su fahimci wani abu da ga gare su.

Duk mazan abokan nan nasu duk abokan Farouk ne sai mai hoton da Tahir ya dauko wanda zai wa Amarya da ango pic and videos.

Sallah su ce ta tsayar da hirar tasu, suka ne me guri suka zauna, ita kuwa kan Fatima a kasa tayi masifar kyau gashi sai wani kamshi take yi.

Su Hafsah ne suke tambayar Fatima wane ango murya kasa kasa dan jalil da Jamal suke kallo dan sun san dai acin su ne.

Tahir ne ya farah addu'a sannan aka shiga magan ganu. Hafsah ta dago tace wa Farouk wai yaya Farouk ina angon yake ne.

Farouk suka saka dariya ya ce Amarya ta nuna maku Ni bana gane su, Nan fa kowa ya ce haka ne.

Ta sar da Fatima sukayi sannan jalil da Jamal suka tashi suna suna fuskantar ta aka shiga video ana cewa ta nuna shi. Wanda ita kanta tasan karya take yi tayi hakan, dan bazata iyya ba dan bata gane suba. Amma sbd karta yarfa kanta a hankali ta Farah tafiya zuwa gaban su. Mai pic ya ce ki tsaya kiji zaki rungume mijin naki ne kinga ne ta daga mashi kai.

Tafiya take tana kallan  su suma ita suke kallah amma tafi gazgata Jamal ne a matsayin jalil da Jamal ya fuskanci shi take nufa sai ya daga mata girah batare da kowa ya an karah ba aikuwa ta faɗa jikin Jalil nan fa guri aka saki dariya. Shima haka ya rungume ta a jikin shi yana sakar mata murmushi mai k'ayatarwa, ya farah mata magana a kunne kinyi matukar kyau matata ked'in ta dabance my love kin hadu sosai, na godewa Allah da ya bani ke a matsayin mata, my love. Ubangijin ya wanzar da zaman lafiya a tsakanin mu mata ta.

Duk jikin ta ya yi sanyi tabbas tayi sa,ar miji, ga kuma wata nutsuwa data shiga jikin ta lokacin ɗaya.

Hatta Farouk sakin baki ya yi yana kallan su, inda kasan wasu masoyan da suke farincikin mallakar junan su. Kai Alhmdllh ko yan zu nasan yar uwar zata samu farincikin a wajen jalil.

Tom a dago haka masoya. Cewar Tahir da Hafsah.

An sha pics cikin burgewa da nuna kaunar juna Alhmdllh inda su Hafsah da su Khadijah da sauran 'yan matan wajen suke ta nuna wa Jamal sosai yana basarwa.

*Kano*

Yau she ne ranar karin haihuwa Jawad sanda shi kan shi ya sha,afa da ranar sai da safe ne yaga MTN sun turah masa sakon sannan ya ankarah, amma shi a nashi lissafin wannan bata zama wata muhimmiyar rana a gare shi ba, dan Rayuwarsa ce ke tafiya. Dan Allah ya kirah mai gadin Company yace zai turah masa da kudi dan Allah ayi abinci a raba sadaka.

Ubangijin ya k'arah masa shekaru masu albarka, amma ba tare da ya faɗa masa manufar hakan ba

Ya kashe wayar ya cigaba da harkokin gaban shi.

Jalilah ce ta shigo dakin fuska dauke da farinciki tace yaya Jawad murnar karin shekara, kallan ta ya yi fuska ɗauke da murmushi yace au murna ki kemun.

Itama murmushi tayi ta ce wish you rayuwa mai albarka and mace ta gari da 'ya'ya masu albarka .

Dan jan kuma tun ta ya yi sannan ya ce ngd my dear sister. Tare da ke my dear ya bani mace ta gari mai kamar ki da kyawun zuciya irin ta ki. Axuciyar sa yace ba irin ta mugun mahaifinki ba.

*Kaduna*

An shirya komi Alhmdllh kuma a yau ne Amarya zata tafi dakin mijin ta.

Kuma Alhmdllh Amarya a yanzu hankalin ta ya kwanta dan yadda Jalil ke nuna mata kulawa Alhmdllh.

Mom ce ta kirah jalil da Jamal ga Fatima ta ce, jalil ina k'arah godiya gareka da karamcin da kamun jalil Ubangijin ya saka maka da mafificin Alkairi. Sai dai ina san amarya ta tare yau a gidan ta da izinin Allah, idan kana ganin babu wata matsala? "Mom gaskiya akwai matsala gidan da muke ginawa nida Jamal bamu kammalah shi ba amma idan ba damuwa akwai na kusa da shi da aka gama zan kama hanyar shi sai mu zauna kafin na kammala nawa in sha Allah".

"Tom ma sha Allah Ubangijin ya sanya alkairi da albarka a auran ku my son. Ina da gida amma na fiso ta kasan ce a naka saboda, hakan shine zata k'arah sanin darajar ka". Fatima kiyiwa mijinki biyayya dan Allah kinga dai halaccin da ya yi mana.

Jamal ya dago da kanshi ya ce dan Allah mom mubar wannan maganar komi ya wuce fa banda tada zance.

Haka kuwa akayi wa a ranar aka kai kayan Fatima. Da dare kuma aka kai Amarya dakin ta. Cikin saka albarka iyaye da 'yan uwan ta. Tayi kuka harta barwa Allah.

Shima b'an garen jalil ya sha addu'a da saka albarka iyaye.

Sannan kuma su Jamal da abokan su suka fito raka shi gidan shi. Har sun fito Jamal ya koma ya dauko wata k'aramar  jaka yasa a bayan mutar suka tafi.

Bakin gidan sukayi parking ko da suka shi gidan shiru da alamar ba kowa a cikin gidan sai amarya.

Madaidaicin falo ne mai dakuna biyu a cikin shi sai kicin. Ko wanne d'aki da ban d'akin  cikin shi, gidan ne madaidaici kuma mai madaidaicin kyau amma ya tsaru.

Sukuwa zama sukayi kan wasu kyawawan kujeru wanda kana ganin su kasan da kudi aka siye su.

Jamal ne ya tabo jalil ya ce tashi kaje ka kira Amaryar mana dare fa yanayi karka manta ba kwana zamuyi ba.

D'akin da ke gaban shiya shiga wanda yana saran ganinta aciki, Amma bai same ta ba, sai kuwa tsayawa ya yi yana kallon wani k'ayataccen  bedroom mai matukar kyau ga wani kan shi mai daɗi da yake ratsa shi.

Fitowa ya yi sannan ya shiga daya dakin bakin shi dauke da Sallah. Ta amsa mashi a nutse gyefenta ya zauna sannan yace ki taso ana jiran mu a falo ta tashi ya rike hannunta cikin salon soyayya yana faɗa mata magan ganu masu dad'i har suka k'arasa falon fuskarta a k'asa sannan kuma a rufe.

Nasiha da addu'oi suka masu sannan suka masu sallah ma tare da aje masu manyan ledoji wanda ko biyar dinsa babu acikin wannan kayan.

Ya raka su bakin kofar gida Jamal ya jawo ɗan uwan na shi ya shiga yi masa nasiha da rikon amanar da aka bashi ya gamsu sosai sannan ya rungume shi hawaye na bin idon shi dan wannan ita ce ranar ta farko da zasu taɓa kwana ba tare ba,  wannan shine lokacin na ɗaya.

Shima rungume shi ya yi zuciyar shi tayi rauni yace kaje yanzu kaga suna jarah na. Kai ma kuma jiran ka tare kabarta ita kad'ai.

Sallah ya yi musu sannan ya wuce gidan cike da kewar d'an  uwa shi.

Kayan ya shigar mata dasu, basu wani b'ata lokacin ba suka Farah ci komi shike bata tare da faɗa mata dad'ad'an malamai  har suka kammala.  Sannan suka yi alwala sukayi sallah . Nan ya shiga tambayar ta abinda ya shafi addini tana bashi amsa yaji dad'in yadda ya sameta da ilimin.

Sannan ya shiga hira da ita, tana kwance a jikin shi, ta kanyi murmushi idan ya faɗi wani abu, da ya fahimci tana tsoran shi yace kije ki kwanta sai da safe. Ta meke zata kwanta yace ki ragye kayan jikin ki dan Allah, Sai dasafe ya fice, ta sauke ajiyar zuciya.

Typing 📲

GAYYA CE!

*Free page*

*Written by*

*Fatima alaramma lafazi*

*(Falaramma)*

https://youtube.com/@fatimaalaramma?si=v_EK6JyH_nkqroPZ

*Sadaukar kar wane ga Sadiq Abubakar CEO din lafazi Allah ya Kara masa lpy, da nisan kwana mai albarka, godiya ta musamman*

💖✨✨✨💞💋💋

Wanan sabon littafi ne, dana farashi kwanan, ina rokon Ubangiji ya bani ikon gamawa lpy,  ina rukun Ubangiji ya bani da mar rubuta abun da mutane zasu amfana dashi wannan kenan.

✨✨✨

Wannan labarin na musamman ne ba gama garin labari bane, GAYYA CE! kuna ji kun San abun sai Wanda ya karan ta, labarin ban dariya da kuma soyayya, tsan tsar cin amana da kuma Butulci, San zuciya da kuma hassada, duk acikin book din GAYYA CE! kunaji kun San ba karya littafin, ina alfahari da ku ges nagode.

PG 1️⃣7️⃣& 1️⃣8️⃣

Ranar Jamal kasa barci ya yi gaba ɗaya ya rasa mai ke damun shi. Yau hatta jamla ta sa ya kasa waya da ita. Ga kuma barci daya kaura ce wa idon shi, dan haka kawai ya yi alwala ya tada sallah yana yiwa ɗan uwan na shi fatan kasan ce cikin farinciki, sbd a zahiri gaskiya yana matuƙar kaunar ɗan uwan sa, sbd yadda yake mashi biyayya koda kuwa baya so.

Washe gari

Ko da asuba da Fatima ta tashi bata ga jalil ba, hakan kuma bai bata mamaki ba, sbd tunda sukayi sallah ma bata karajin motsin shi ba.

Da asuba ne data tashi taji mutsin shi da alama masallaci yaje.

Amarya da sassafe ta tashi tayi wanka ta shirya cikin wata shaddar wadda tasha aiki, ba karamin kyau tayi ba.  Duk da dama Fatima kyakkyawa ce bata da makusa.

Koda ta fito falo bata gan shi ba dan haka ta shige cikin.

Dubawa ta fara yi a nutse ta samu kayan da take buƙata, nan take ta daura musu tea da dankali. Ba wani lkcn ta bata ba ta kammala, ta koma kan gidan ta gyerah shi tsaf sannan ta shiga dakin da yake dan har lokacin ba mutsin shi. Kwance ta tarar da shi yanata barci cikin nutsuwa, a hankali ta k'arasa bakin gadon ta zauna tana kare masa kallo, duk da jikin shi a rufe yake fuskar shi ce kawai a buɗe. Ta jima tana kallan shi daga bisani ta mike ta fita daga d'akin.

D'akin ta takoma ta sake wani wankan sannan ta kuma shirya wa cikin wani tsadadden Les blue tayi daurin ture kaga tsiya inda ta saki gashin ta tabaya  ta feshe jikin ta da turaruka masu dad'i sannan ta fito falon da sauri sbd mutsin da take jiyo wa.

Tana fito wa idan su ya sauka a kan juna.

Suka sakarwa juna murmushi a tare.

Ta kowa ya shiga yi har ya kara so inda take fuskar shi dauke da murmushi yace  morning my beautiful wife. Kasa tayi da kanta sbd irin kallon da yake mata.

"Cikin sarke war murya ta ce morning too my dear husband.

Hannun ta ya ka ma suka kara so falon kan kujera ya zaunar da ita sannan ya ce. My Teema ta dago ta kalle shi ya ce. Daga yau bana san irin wannan gaisuwar kinji ta daga masa kai alamar eh ya ce yawwa.

Yau she ki ka tashi ki kayi aiki  da yawa haka mai makon ki jira na tayaki.

Kai haba yaya Jalil ai aikin ba shi da yawwa, kuma yau she zan barka da aiki ma.

Kalla ta yake sannan ya ce mema naji kin kirani da shi.

"Ta ce yaya Jalil fa na ce ta faɗa a shakwabe tare da turu baki.

Murmushi ya yi mata Sannan yace bana san wannan sunan fa.

"Ta  kuma toru baki, ta ce to  yaya Jalil bata karasa ba ya haɗe bakin shi da nata yana masa Mani irin tsotsa.

Gaba daya jikin ta rawa yake ga kuma wani hawaye da yake biyo idon ta. Jikin ta ya yi wani mugun san yi.

A hankali ya fara sakin bakin nata, ya saka hannu ya dago da kanka yace daga yau idan ki ka kuma fadar haka hum, yan zu tashi muje kimin wanka sai muyi breakfast.

Bai jira abin da zata ce ba yaja hanun ta suka shiga d'aki.

Kai tsaye Toilet ta shiga ta haɗa masa ruwa Sannan ta fito kai a ƙasa ta ce na gama, kallan ta ya yi yace eh amma saura wanka.

Ta ce dan Allah kayi da kan ka kaji, rabuwa ya yi da ita ya shiga wanka sbd ya fahimci a tsora ce take da shi.

Jakar da ta gani a ajiye ta dauko, ta shiga bude ta, wata shadda ta dauko masa white color. Ragowar kayan ta shiga jera mashi a cikin wadirop din dakin sannan ta fito sbd jin a lamun fito warsa.

Fatima yarin ya ce karama wadda ba zata wuce 21 yaes ba. Yarin ya ce mai ilimi Addini da na boko. Yarin ya ce nutsatsiya mai ciki da kuruci da shagwab'a sakamakon ita ce auta a wajen mom dinta.

Shirya wa ya yi cikin kayan da yaga ta aje masa sannan ya fito zuwa falon ya ganta a zau ne da alama tuna ni ya keyi dan ya fahimci bata masan yazo wajen ya zau na ba.

Hannun shi ya daura kan fuskar ta, ya ce my dear tuna nin mai ki keyi. Bai k'arasa magana ba yaga hawaye na zuba daga idon ta, ta faɗa kirjin shi ta fashe da kuka.

Cikin tausayi da girmama wa yake shafa bayan ta ya farah magana a hankali ya ce dan Allah my dear ki faɗan mai nayi miki har na saki kuka haka ko kina so na kasa yafewa kai na ne.

Cikin hanzari ta dago da kanta daga jikin shi tace my husband baka mun komi ba, asalima jin dadi kasan ce wa da kai ne ya sani hakan.

"Kai din ka kasan ce haske ne a gare ni".

kuma abun alfaharin na. kai ɗin muradin ko wacce uwa ne. Kuma alfaharin co wacce 'ya, ina sanka miji na ina kuma alfahari da samunka a matsayin miji na. Ubangijin ya bani ikon yimaka biyayya.

Sosai shima ya rungume ta ya ce kema haka my dear. Ubangijin ya sanya alkairi da albarka a auran mu ya bamu zuri,a d'ayya ba.

Amma fa ki sani ni 'yan uku nake so.

Dariya tayi ta ce kai my husband, ai nayi yarin ya bazan iyya haihuwa yan zu ba, kuma ciki na bazai iyya daukan uku ba fa, ta ƙare maganar cikin wata irin murya.

"Au haka ma zaki ce my dear tom Allah ya kai mu anjima zamu gani.

Ya kare maganar yana mata dariya sbd ganin yadda ta hade fuska.

Ta shi tayi ta kawo musu breakfast, wanda gaba ɗaya sun ma man ce suna jin yinwa, suka Farah ci yana bata a baki shima yana ci, Ya nata mata santi sannan suka kammalah ta kwace kayan ta kai kichin, ya taya ta da wasu.

Tare suka gama wanke kayan, cikin farinciki da jin daɗi.

Falo suka dawo suka zau na, suna hira lokacin har 12:9 tayi, wayar sa ya d'auko ya farah dan na number Jamal, ita kuma Fatima na kwance a kafadar sa.

Bugu ɗaya ya dauka.

Bakin shi ɗauke da Sallah ma yace Ango kasha kamshi.

"Jalil ne ya amsa masa yana dariya ya ce  kai Jamal a kwai ka da tsokana.

"Jamal ya ce danaji shiru ai nace ba zaka kirah mu ba.

"Dariya jalil ya yi yace ni a wa zank'i  kiran ka.

"Jamal ya ce fatan dai baka wahalar mun da k'anwar ba ko?

"Dariya jalil ya yi yace ummm.

Da ta fahimci hirar ta su sai ta mike ta shiga d'aki.

"Jalil ya ce kadai san ni da tausayi.

"Jamal ne ya kwashe da dariya yace a ina, idan kuma haka ne to ka barta tayi one week mana.

"Jalil cab ai wllh jiyan ma nayi kokari, dan daga kyau na gama hakuri.

"Kai mugu, wllh ka bi mana k'anwa  a hankali ta,

" Kai dai kawai sai abun da kuka ji.

Da haka dai suka yi ta hira suka canza akalar maganar zuwa wata hirar.

Sannan sukayi sallah ma.

Haka suka wani suna hira basuyi wasu baki ba, karfe 2:00 mom ta aiko direver ta ya kawo masu abinci. Suka kirata suka mata godiya ta tambayi Fatima tace  Alhmdllh sai godiyar Allah.

Da yamma karfe hudu ya ƙarah shirya wa sannan ya yi mata sallah ma ya fita, har bakin kofar ta rakoshi tana ta mashi addu'a, da fatan alkairi tana a gaida  inna da jawahir kuma yan she zasu zo.

*KANO*

Haka ita ma Ammy ba,a barta a baya ba wajen yiwa ɗan nata sada,ka da addu'a fatan alheri da samun mace ta gari kamar yadda suke fata.

Yan zuma zau ne ya ke kusa da ita yana mata Magana cikin nutsuwa, tana bashi amsa.

"Ammy Jawad kasan wani mafarki da nayi jiya.

" A'a Ammy ban sani ba sai kin faɗa"

Wallahi nayi mafarki kayi aure har an kai maka matar kuma kuna cikin farinciki.

"Murmushi Jawad ya yi mata".

"Ammy kawai sbd kina muradin hakan ne yasa amma, ai in sha Allah zanyi noma kamar yadda ki ke fata."

Allah yasa amma gaskiya jiya na kasance cikin farin ciki mara misaltuwa bana jin ko wacce irin damuwa a tattare da ni".

"Alhmdllh Ammy Allah yasa Alkairai".

"Ta ce  Ameen".

Jalila ce tayi sallah ma ta shigo d'akin gyefen Jawad ta zauna.

"yaya ina wuni"

"Lpy lau Alhmdllh my dear sister"

Amma dama tuni sun gaisa tun dazu, sbd dazun ta shigo baya nan.

Jalilah dazu Tahir yazo abokin Jawad yake faɗan wata magana, wato Jalila ke da yayin ki bazaku yiwa kan ku faɗa ba kuyi aure, aure fa shine mutum cin mutum. Ta kare magana ran ta a ɗan b'ace.

"Ammy ni nafi so idan yaya Jawad ya yi ni ma sai nayi tunda kin ga shi ne babban, kuma ni har yanzu ban samu wanda ya yi min ba.

"Ammy ai ke da yayan ki ba zaku taba samun wanda ya yi maku ba".

" Wallahi zan haɗa ku da Papan ku, nagaji da rashin jikoki a gaba na.

*Kaduna*

Yau ta kama ranar Monday kwana ɗaya da dawowar su Dad da mom din jamlah, daga Lagos, sbd a can take komi na cikin jikin ta wanda a yan zu ya fito sosai. Dar baya barin ta yin komi inda kuma jamlah ma bata bari sosai take farincikin da cikin, ga kuma wani kaunarsa da take ji.

Ita kuwa mom sosai take jin kunyar cikin a cewar ta wai tayi girma da haihuwa wanda ba ko wane ma yasa akwai cikin ba, sai shakikan kannan ta da yayyen ta sai kawar ta.

Dad ne ya shiga falon ya samu su Jamal a zaune tana dan na wa mom ƙafa, suna tabba hira kadan kadan.

